JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA — 16 Rabi'ul Awwal, 1443
MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI — 22 Oktoba, 2021

(١)

## ANNABI (SALLALLAHU ALAIHI WA ALIHI WA SALLAM)

## CIKAKKEN MALAMI MAI TARBIYYA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Saboda rahama daga Allah ne, ka zama mai sauƙin kai a gare su)** [Ali Imran: 159]. Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) babban abin koyi ne ga ɗaukacin bil'adama wajen ingantaccen bayar da tarbiyya, da karantarwa mai nagarta, (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) malami mai tsananin tausayi, mai kuma tarbiyya ne cikin hikima, yana tafiyar da mutane cikin sauƙi, yana kuma karantar da su ta hanyoyin da suka fi dacewa, hasali ma shi da kansa (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ne yake cewa: **(Lallai Allah bai aiko ne a matsayin mai matsi da tsanantawa ba, ya aiko ni ne a matsayin malami mai sauƙi)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Sauƙi bai taɓa shiga cikin kowane irin abu ba, face ya ƙawata shi, ba kuma a taɓa cire shi cikin kowane irin abu ba, face ya munana)**.

Duk mai duba na lura a cikin tarihin Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) zai ga cewa: lallai shi ne fiyayyen malami ga sahabbansa, da ma ɗaukacin bil'adama, kuma zai ga cewa Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya fi kowa

tausayin halittar Allah, ya fi kowa jinƙan mutanen da yake karantarwa, da waɗanda yake koya masu ladabi da tarbiyya, da waɗanda yake sanya su a gwadabe na gari, ga Sayyiduna Mu'awiyya Bn al- Hakam (Allah ya ƙara yarda da shi) nan yana cewa: wani lokaci ina sallah a bayan Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai wani daga cikin mutane ya yi atishawa, sai na ce masa: "YarhamukalLah", sai mutane suka yi mini ƙuri da idanuwansu, sai na ce: ikon Allah, me kuma na yi da kuke kallo na? sai suka koma dukan cinyoyinsu da hannuwansu; da nufin in yi shiru, da na ga suna ƙoƙarin sanya ni in yi shiru, sai na yi shiru, lokacin da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya gama sallah –iyaye na biyu fansa ne a gare shi- wallahi ban taɓa ganin malami kafin shi, da bayan shi, da ya kai shi iya koyarwa ba, bai ƙyare ni ba, bai kuma doke ni ba, bai kuma zage ni ba, abin da ya ce kawai shi ne: **(Wannan sallah ce da maganganun a tsakanin mutane bai halatta a cikinta ba, abin da ake yi a ciki kawai shi ne: Tasbihi, da Takbiri, da karatun Alƙur'ani)**.

An ruwaito Hadisi daga Abi Umama (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Wani matsashi saurayi ya zo wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), sai ya ce: Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), ka yi mini izinin yin zina!. Sai mutane suka yi masa cã, suna hantararsa, suka ce: yi mana shiru. Sai ya ce: **(Ku matso da shi)**, sai ya ɗan gusa kusa da shi, ya ce, sai ya zauna: Sai ya ce: **(Yanzu kana son a yi haka da mahaifiyarka?)**, ya ce: a'a wallahi, Allah ya sanya ni in zamo fansarka. Ya ce: **(Haka ma mutane ba sa son a yi da mahaifansu mata)**, ya ce: **(Yanzu za ka so a yi da 'yarka?)**, ya ce: a'a wallahi, Allah ya sanya ni in zamo fansarka. Ya ce: **(Haka ma mutane ba sa son a yi da 'ya'yansu)**. Ya ce: **(Yanzu za ka so a yi haka da 'yar**

**uwarka?)**, ya ce: a'a wallahi, Allah ya sanya ni in zamo fansarka. Ya ce: **(Haka ma mutane ba sa son a yi da 'yan uwansu mata)**. Ya ce: **(Yanzu za ka so a yi haka da 'yar uwar mahaifinka?)**, ya ce: a'a wallahi, Allah ya sanya ni in zamo fansarka. Ya ce: **(Haka ma mutane ba sa son a yi da 'yan uwar mahaifansu mata)**. Ya ce: **(Yanzu za ka so a yi haka da 'yar uwar mahaifiyarka?)**, ya ce: a'a wallahi, Allah ya sanya ni in zamo fansarka. Ya ce: **(Haka ma mutane ba sa son a yi da 'yan uwan mahaifiyarsu mata)**. Ya ce: sai ya ɗaura hannunsa a kansa, ya ce: **(Ya Ubangiji ka gafarta masa zunubinsa, ka kuma tsarkake zuciyarsa, ka kuma kiyaye farjinsa)**. Daga wannan lokacin matashin bai sake waigawa zuwa ga komai ba.

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Duk wanda yake duba ta lura zuwa ga rayuwar Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), zai ga cewa a koda yaushe yana sassauya salonsa na kira zuwa ga Allah, da na karantarwa, inda yake amfani da hanyoyin ƙwarewa wajen isa zuwa ga mutane ta hanyar da'awa; saboda ya samu ya shiga cikin zuciya da hankalin mai sauraro, a wasu lokuta yana amfani da harshen lissafi; saboda ya kusanto wa da ƙwaƙwale ma'anonin da yake son isarwa, kaman inda (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yake cewa: **(Abubuwa guda uku kam, duk wanda ya same su ya ɗanɗani garɗin imani: Ya zama ya fi son Allah da Manzonsa**

**akan duk wani da ba su ba, idan kuma zai yi soyayya da wani ya so shi saboda Allah, ya kuma ƙyamaci komawa cikin kafirci bayan Allah ya tseratar da shi daga ciki, kaman yanda yake ƙyamatar kada a jefa shi a cikin wuta)**.

A wasu lokuta kuma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana karantarwa ne ta hanyar buga misalai da suke ƙara kusanto da abu, da ƙarin haske akansa, kaman inda (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yake cewa: **(Misalan aboki na gari, da abokin banza, kamar mai sayar da turaren almiski ne, da mai hura zuga- zigi, shi mai sayar da almiski, ko dai ya ba ka kyauta, ko kuma ka saya a wurinsa, ko kuma ka sami ƙamshi mai daɗi, shi kuma mai hura zuga- zigi, ko dai ya ƙona maka tufafi, ko kuma ka kwashi ƙauri mara daɗi)**.

A wasu lokuta kuma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana amfani da salon jefa tambayoyi; saboda ya jawo hankulan masu sauraro, da sanya masu shauƙin sauraron amsa, kaman inda yake cewa: **(Shin ko ku san wane ne muflisi?)**, sai suka ce: Ya Manzon Allah, muflisi a cikinmu shi ne: shi ne wanda ba shi dukiya, da kayan alatu na duniya, sai (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Muflisi a cikin al'umma ta shi ne wanda a ranar alƙiyama zai zo da sallarsa, da azuminsa, da zakkarsa a cike, amma kuma ya zagi wannan, ya kuma yi wa wancan ƙazafi, ya ci dukiyar wannan, ya zubar da jinin wancan, ya daki wannan, a biya wannan daga cikin kyawawan ayyukansa, wancan ma daga kyawawan ayyukansa, har sai idan kyawawan ayyukansa sun ƙare kafin a gama biyan kura-kuran da ya tafka, sai a ɗauko zunubansu a jibga masa, sannan a jefa shi cikin wuta)**.

Haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yakan zaɓi ranaku, da lokutan da suka dace da karantarwa, gami da shiryatarwa; saboda ya sanya ƙwaƙwalen masu sauraro cikin nishaɗi, da kuma kawar masu da ƙosawa, Sayyiduna Abdullahi Bn Mas'ud (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yakan ware mana wasu kwanaki ne na wa'azi, gudun kada mu ƙosa.

Lallai muna matuƙar buƙatar koyi da ɗabi'un Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), muna karantarwa, muna kuma neman karatu, saboda mu yaɗa saƙonsa, mu kuma bayyana shiriyarsa, da sunnoninsa.

**Ya Allah Ubangiji ka azurta mu da ilimi, gami da ladabi, ka shiryatar da mu zuwa ga yin ado da kyawawan ɗabi'un Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam).**